Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, Daivi Rodima-Taylor, and Rebecca Shereikis. 2022. "Nana Asmāʾu: Admonition." https://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/hunwick-95-3-nana-asmaau-waazi/.

**Nana Asmāʾu: Wa'azi**

[Page 1]

Bismi l-Lāh al-Raḥmān al-Raḥīm. Ṣalla l-Lāhu ʿalā l-Nabiyi l-Karīm

Shiʿru Asmāʾu bint Shaykh ʿUthmān, raḍiya l-Lāhu ʿanhumā.

Na fa gode Ubangiji na Raḥīmi

Wanda yayyoni mai sarauta Karīmi

Wāhidun shi kaɗai shi adda iko

Babu farko ga wanda yaffara komi

Mai fa ji na ḥaqīqatan mai ganina

ʿĀlimul Ghaybi mai sanina Ḥalīmi

Sani fa ji nai ḥaqīqatan babu kunne

Har ganinai fa ba da idanu ka Fahīmi

Bada ko gaskiya garai tabbace shi

Babu Sarki ḥaqīqā sai Shi Karīmi

Bada ko gaskiyar Muhamman ma'aiki

Don ka zama mumini ka zama ko salāmi

Bar fa biɗa ka kamma hanya

Ita ka isshe ka har ga Daru l-Salāmī

Don fa tuba ka bada tsarki ga bawa

Dagga zunubi shi tsira ga shiga Jāhīmī

Tsare fa tsarkin wuɗu'u wankan janaba

Inda shari'a babu ciwo ga jismi

Inda ciwo ka taimama don ta'ala

Allah yassauƙaƙa ma bawa ʿAlīmī

Mai fa aikin da yaffi so mai hukunci

Duk ga aikinsa mai Irādā Ḥakīmī

Duk mu zam ko biɗa ga Allah Sarki

Gafara ko mu samu yarda ʿAẓīmi

[Page 2]

Dawwamamme ḥaqīqatan ba shi mutuwa

Sarmadan dāʾiman shi ke bi dawami

Duk ku saurara ƴan uwa za ni wa'zu

Don ku amfana wa'zu shi adda tammi

Ƴan uwa duk mu tuba domin fa tuba

Affa ƙofar isa ga Sarki Raḥīmī

Zanka sadaka da nāfilā ka yi ṣalāti

Bisa fiyyayenmu Sidi shi Imāmī

Zamka dhikri da safe hakana marece

Zanka tashi cikin dare Qiyāma

Son fa Qurʾāni affa son Sarki

Har ma'aiki riƙe tutut kullu yawmi

Ka ji hanya ta bi na Allah ḥaqīqa

Wanda yabbi ta ya fa zan Muṣtaqīmi

Hatta mata ku bar fita sai lalura

Ɗai biɗa ci da tambayowa ga ʿilmi

Nan ga addini biɗar sanin farḍu-ʿaynin

Shi ka sa mace ko fita babu komi

Duk ku tuba ku zamka ɗa'a ga mare

Duk ku zam bin ma zanku ga ḥukmi

Duk ku zam lullubi ku ko tsaraici Allah

Kada ku sa kanku gobe ga wutar Jahīmī

Wadda duk taƙƙiya ba ta sami lada

Ta yi rubushin rabo ga Sarki Raḥīmī

Na yi waƙa ta wa'zu domin ku karɓa

Don ku 'amfāna niyyi jama'ar Musulmi

Na cika, na yi godiya, nai ṣalāti

Bisa fiyayye da ṣaḥbu duk in salāmi

Ayi ƙida ko na ramzu hijrar fiyayye

Kana bishrun mu sami nasrar Karimi

Alḥamdu li l-Lāhi waḥdahu

Ṣalla l-Lāhu ʿalā ḥabībīhī